SIFFAR WANKAN JANABA

Daga Maimuna Uwar Muminai - Allah Ya yarda da ita - ta ce : Na ajiye wa annabi - tsira da a mincin Allah su tabbata agare shi - ruwan wanka, sai na kare shi da tufafi, sai ya saka a hannayensa, sai ya wankesu, sannan ya zuba da damansa akan hagunsa, sai ya wanke gabansa, sai ya goga hannunsa a kasa, sai ya shafe shi, sannan ya wanke shi, sai ya kuskure baki ya shaƙi ruwa, ya wanke fuskarsa da zira'in hannunsa biyu, sannan ya zuba a kansa sai ya kwaranyo ruwan akan jikinsa, sannan sai ya gusa kadan, sai ya wanke diga-digansa, sai na ba shi tufafi bai karɓa ba, sai ya tafi alhali yana kakkaɓe hannayensa.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Uwar muminai Nana Maimuna - Allah Ya yarda da ita - ta bada labari game da siffar wankan annabi - tsira da a mincin Allah su tabbata agare shi - na tsarki, lokacin da ta ajiye masa ruwa dan ya yi wanka da shi, kuma ta kare shi da labule, sai annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya aikata abinda ke tafe: N farko: Ya zuba ruwa a hannayensa sai ya wanke su kafin ya shigar da su cikin abin wanka. Na biyu: Ya zuba ruwa da hannunsa na dama akan hannunsa na hagu sai ya wanke gabansa; dan tsarkake shi daga abinda ya maƙale na alamar janaba. Na uku: Ya bugi ƙasa da hannunsa sai ya shafe shi sannan ya wanke shi dan ya gusar da ƙazanta daga gare shi. Na huɗu: Ya kurkure baki; ta hanyar shigar da ruwa a cikin bakinsa ya motsa shi ya kuma kurkure shi sannan ya zubar da shi, sai ya shaƙi ruwa; ta hanyar da ya shigar da ruwa a cikin hancinsa da nunfashinsa, sannan ya fitar da shi dan ya tsarkake shi. Na biyar: Ya wanke fuskarsa da zira'insa biyu. Na shida: Ya zuba ruwa a kansa. Na bakwai: Ya zuba ruwa a sauran jikinsa. Na takwas: Ya juya daga gurinsa sai ya wanke diga-digansa a wani wurin daban ta inda bai wankesu ba kafin nan. Sannan ta kawo masa wani mayafi dan ya tsane da shi, bai karɓa ba, sai ya fara shafe ruwan jikinsa da hannunsa yana karkaɗe shi.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/3310